*18.* Waɗannan ne ma'abũta albarka[1]

أُولَٰٓئِكَ أَصۡحَٰبُ ٱلۡمَيۡمَنَةِ ١٨

*19.* Kuma waɗanda suka kãfirta da ãyõyinMu, sũ ne ma'abũta shu'-umci[2]

وَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِـَٔايَٰتِنَا هُمۡ أَصۡحَٰبُ ٱلۡمَشۡـَٔمَةِ ١٩

*20.* A kansu akwai wata wuta abar kullewa.

عَلَيۡهِمۡ نَارٞ مُّؤۡصَدَةُۢ ٢٠

## SŨRATUSH SHAMS سُورَةُ الشَّمۡسِ

Tana karantar da cewa idan azãba ta sauka a kan mutãne, takan shãfi mai laifi da wanda bã shi da laifi daga cikinsu.

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

*Da sũnan Allah, Mai rahama, Mai jin ƙai.*

*1.* Ina rantsuwa da rãnã, da hantsinta,

وَٱلشَّمۡسِ وَضُحَىٰهَا ١

*2.* Kuma da wata idan ya bi ta.

وَٱلۡقَمَرِ إِذَا تَلَىٰهَا ٢

*3.* Da yini a lõkacin da ya bayyanã ta.

وَٱلنَّهَارِ إِذَا جَلَّىٰهَا ٣

*4.* Da dare a lõkacin da ya ke rufe ta.

وَٱلَّيۡلِ إِذَا يَغۡشَىٰهَا ٤

*5.* Da sama da abin da ya gina ta.

وَٱلسَّمَآءِ وَمَا بَنَىٰهَا ٥

*6.* Da ƙasã da abin da ya shimfiɗã ta.

وَٱلۡأَرۡضِ وَمَا طَحَىٰهَا ٦

---

(1) Ko kuwa waɗanda ake bai wa takardunsu ga ɗãma, a Lãhira.

(2) Ko kuwa waɗanda ake bai wa takardunsu ga hagu, a Lãhira.

*7.* Da rai da abin da ya daiɗaita shi,

وَنَفۡسٖ وَمَا سَوَّىٰهَا ٧

*8.* Sa'an nan ya sanar da shi fãjircinsa da shiryuwarsa,

فَأَلۡهَمَهَا فُجُورَهَا وَتَقۡوَىٰهَا ٨

*9.* Lalle ne wanda ya tsarkake[1] shi (rai) yã sãmi babban rabo.

قَدۡ أَفۡلَحَ مَن زَكَّىٰهَا ٩

*10.* Kuma lalle ne wanda ya turɓuɗe[2] shi (da laifi) ya tãɓe.

وَقَدۡ خَابَ مَن دَسَّىٰهَا ١٠

*11.* Samũdãwa sun ƙaryata (Annabinsu), dõmin girman kansu.

كَذَّبَتۡ ثَمُودُ بِطَغۡوَىٰهَآ ١١

*12.* A lõkacin da mafi shaƙãwarsu ya tafi (wurin sõke rãƙumar Sãlihu),

إِذِ ٱنۢبَعَثَ أَشۡقَىٰهَا ١٢

*13.* Sai Manzon Allah ya gaya musu cewa, "Ina tsõratar da ku ga rãƙumar Allah da ruwan shanta!"

فَقَالَ لَهُمۡ رَسُولُ ٱللَّهِ نَاقَةَ ٱللَّهِ وَسُقۡيَٰهَا ١٣

*14.* Sai suka ƙaryata shi, sa'an nan suka sõke ta. Sabõda haka Ubangijinsu Ya darkãke su, sabõda zunubinsu. Sa'an nan Ya daiɗaita ta (azãbar ga mai laifi da maras laifi).

فَكَذَّبُوهُ فَعَقَرُوهَا فَدَمۡدَمَ عَلَيۡهِمۡ رَبُّهُم بِذَنۢبِهِمۡ فَسَوَّىٰهَا ١٤

*15.* Kuma bã ya tsõron ãƙibarta (ita halakãwar).

وَلَا يَخَافُ عُقۡبَٰهَا ١٥

---

(1) Karɓar imãni da aiki da abin da ya ƙunsa tsarkake rai ne.

(2) Kafirci turɓuɗe rai ne da zunubi.